"A wanan zamani, maza na kallon mata a matsayin abokan biya bukata kawai. Meyesa zaki fitar da tsiraicin ki ga mutanen da ba muharamman ki ba? *Hijabi* shine kariya ga mutuncin mace kuma kariya ga mutumin da yake muharammin ki. Ina gamin in har mata za su bi ka'idar suturar musulunci, awaitar ayyukan assha, cin zarafi da fyade da sauransu za su ragu sosai etc. Sanya *hijabi* na kara min kwarjini a matsayi na ta ya mace, bai kuma takura min a wurin ayyukana na yau da kullum." Inji Malama Salva I Rasool, mai sana'ar zane.

"Ban dade da musulunta ba, saboda haka zan iya bada gamsasshen sutura a rayuwa ta tsarin musulunci da wanda ba ta musulunci ba. Ina sane da dai'un mutanen yammancin duniya dangane da *hijabi* da cewa yana takura wa yancin mata. Fahimta ta dangane da *hijabi* da kuma bincike na a addinin musulunci ya bani damar fahimtar cewa al'amarin bah aka yake ba. Wasu lokuta mutanen da ba musulmai ba kan zuba min ido, amma a cikin *hijabi* sukan karama ni. Ban taba samun matsala dangane da aiki na ba, bana kuma fuskantar wasu matsaloli ko manganun banza daga maza. Na fi samun natsuwa idan ina sanye da *hijabi*. A yanzu na fahimci zan iya hulda da wasu a matsayi na mutum ba tare da cutarwa dangane da suturar da nake sanye da ita ba. Ko a tasha ne mutnen banza kan kauce min. Fahimtar cikakkiyar kariya da *hijabi* a musulunci ke bada wa da kuma sanin cewa ya kan kara min kima da kariya a idon mutanen da nake hulda da su. Sanin muhimmancin *hijabi* yasa ba zan iya rayuwa ba tare da shi ba. Na kan shiga jama'a a matsayin cikakkiyar musulma – tunatarwa agare ni da duk masu gani na zan ba ma kai na rayuwa ta mutunci da kamala. Na zaba bin umurnin Allah a kowane hali. Yadda mutane suka san mata masu kula da coci, haka ni ma suka san ni. Ko da basu fahimci suturar da ba a saba da ita ba a Amruka, sukan nuna sha'awar su da wanda bai shakkar rayuwa a mutunce." Inji Malama Diana Beatty, Malamar makaranta.

"Na ji ina son sa *hijabi*. A gaskiya kalmar 'so' ba shi yada ce ba saboda bai ba da ma'ana ba. Ina kaunar sa. A rayuwata na farko a matsayi na ba'amrukiya, na ji cewa lalle yanzu jiki na nawa ne. A yanzu zan iya cewa, na samu cikakkiyar kamala ta mutuntaka a matsayi na ta ya mace. Na fahimci ana bani cikakken kula, da mutunci. Na kuma fahimci shakku daga maza matasa wajen tunkara ta da nufin magana ko wani abu. Yadda wanan al'amari ya bayyana karara shine yadda maza ba su bi na da idanuwan su idan ina wuce wa. *Hijabi* ne ya isar min da wannan sakon, ko ba yawa amma yana dauke da ma'ana mai karfi …" In ji wani ba'amruke wanda ba musulmi ba a wurin taron *Scarves for Solidarity* da ya biyo bayan 11 ga watan satumba yadda aka ciro a wasikar zuwa ga… San Fransisco. A mujallar (Chronicle) tara ga watan mayu 2002.

**Idan ana neman kari akan Musulunci,a tuntubi**

***http://al-islam.org/faq/***

*v1.0*

*"Kace wa muminai maza su runtse daga ganinsu, kuma su tsare farjojinsu…… kuma kace wa muminai mata su runtse daga gannansu kuma su tsare farjojinsu kuma kada su bayyana kawarsu face abinda da ya bayyana daga gareta………*

(Qur'an: Sura 24, Aya 30-31)

# Me Yasa Musulmai Ke da Dokar Sa Sutura?

Musulunci bai hana cudanya tsakanin maza da mata ba, sai dai ya shimfida wasu ka'idoji na mu'amala a tsakaninsu ta yadda kowa zai mutunta juna. Mu'amala a musulunci yana tattare ne da kyawawan halayya da mutunci da kuma wata ka'idar sutura ga mata, wanda take tattare da lullube jikin ta.

## Ku Runste Daga Gannan Ku Saboda Kyautata Zukata

Hikimar dake tattare da abin da akafi sani da suna *hijabi* – sutura a musulunci – ya samo asali ne daga kare hankalin mutum daga duk abinda ke iya nakasa mutuncin shi. Imam 'Ali, kani da kuma surukin manzon Allah (Amincin Allah su tabbata a gare shi da iyalen gidansa), yace,

*"Ido shine mahangar zuciya kuma manzon kwakwalwa; saboda haka kauda idanun ka daga ababen da basu da kima a musulunci..."*
Fitilar Hanya

A wanan zamani, gababen sadarwan mu a lillube suke da abubuwan daukan hankali na gani, saurare da shaka. Musulunci ya nuna mana hanyoyin da zamu kare hankulan mu daga ababen sha'awa saboda su kan tasirantu a kawukanmu da haka ya shafi mutuntakan mu. Kanaiya tunawa da kakar ka wanda tsawon lokaci baku sadu ba daga jin kanshin turaren daka san ta da shi, harbe harben bindiga na bukin hawan salla na iya sa ka tsamanin yaki ake yi; hangen mace kyakkyawa sanye da tufafi mai nuna tsaraici na iya ta da hankalin mutum.

Idan muka gan wata/wani yana rashin da'a, laifi ko cin mutunci, duk da cewa ba kai/ke ke yin laifin ba, mutum yakan damu a ransa. Kowa ya tuna da laifukan da yake yi lokacin da yake karami yakan damu a ransa. Mutunci madara ne, in ya zube ba'a kwashewa.

A musulunci, ba wai iyaye suke kula da tarbiyyar yayansu bane kawai, su ma matasa wajibi ne su kula da kawukanansu wurin tarbiya, sabawa wa haka na iya samar wa lalatacciyar al'umma.

Saboda haka, babbar hikimar dake tattare da *hijab* shine na kariya da kiyaye mutuncin mata ta ko wace hanya a rayuwa. Ya wajaba damu kare kanmu daga kale kallen maza ta sanya sutura da zasu kare mana mutuncin mu.

## Cikakkiyar Kula da sa Hijabi.

Alkur'ani mai girma ya umurce mu da sa sutura a musulunci kamar haka:

*"Kace wa muminai maza su runtse daga ganinsu kuma su tsare farjojin su. Wanan shine mafi tsarki a gare su. Lalle Allah mai kididdigewa ne ga abinda suke sana'antawa. Kuma kace wa muminai mata su runtse daga gannansu, kuma su tsare farjojin su kuma kada su bayyana kawarsu face abinda ya bayyana daga gare ta kuma su buga mayafansu akan wuyan rigunansu kuma kada su nuna kawarsu face ga mazansu ko [Muharramansu wanda Alkur'ani ya bayyana]..."*
Surah 24, Aya 30-31.

Dalilin wannan tsarin shine kare mutuncin mata da maza a lokacin mu'amala.

- Da farko, maza ne ya kamata su jagoranci kare mutuncin mata. Bai kamata a ce sun taimaka ko ba da dama a wurin cin zarafin ya mace ba. Ya kamata a ce sun kalli mace da mutunci da kiyayewa wajen kai zuciya nesa a lokacin hulda.Ya wajaba su sa sutura masu mutunci da kiyaye hulda a wuraren da bai kamata ba.
- *Hijabi* baya hana hulda tsakanin maza da mata ba wajen karatu, aiki, taimakawa juna da sauransu.Idan aka kiyaye mutuncin hijabi, irin wanan hulda zai faru da aminci ba tare da zargi ba.
- Ya kamata mata su kare mutunci, suyi hulda da maza a mutunce. Kada su kaskantar da mutuncinsu da kadifiri da kisisina ta yadda za su jawo hankalin maza in suna tare da su.
- In suna tare da mazajen da ba danginsu bane, ya wajaba mace ta kasance da suturar da zai kare dukanin jikinta. Malaman musulunci sun tabbatar da cewa wajibi ne kowace mace ta lullube dukkan jikinta banda fuska da hannu. Mata musulmai na cika wannan ka'idojin ta hanyar sanya hijabi.
- Bukatan sutura na kamala ya saba tsakanin jinsi saboda sabanin halitta da sha'awa tsakanin mata da maza. Za'a iya fahimtar wannan sabanin a kasashen turai a inda mafi akasarin mata basu damu da karanta mujallun batsa ko karuwanci in ka kamanta su da maza da ke aikatan hakan.
- Sabanin ra'ayin wasu, hijabi ba al'amarin kaskanci ko kuma tilasci akan ya mace bane, banbanci kawai tsakanin maza da mata a gaban Allah shine taqwa, Ba'akan iya banbance halayya da zahirin al'ummar da ta inganta suturar taba sai dai hanyar ilimi da kamalar mutum.
- Dokar sa sutura a musulunci baya takura wa mata ko hana masu walwala, fadin ra'ayi, nemen ilimi, kula da lafiya da wasu yancinsu na yan adam sai dai yana taimakawa ne wajen gina ingantacciyar al'umma da rage ayyukan assha kamarsu fyade da tozarci saboda yiwuwar aikata wa'yannan laifuka yana da wiya idan an kiyaye sa *hijabi* . Kiyayaye sa *hijabi* bangare ne na rayuwa a addinin musulunci wanda in har aka bi shi sahu da kafa zai tabbatar da mutuncin maza, mata da al'umma gaba daya.

## Meye Matan Musulmai ke Tsammani Dangane da Hijabi?

"Nakan ji wata kariya ta musamman a tare dani. Mutane kan kalle ni da muhimmanci kuma na kan jini da kwarjini in ina kan hanya." Dr. N.Z. Vakil, M.D. Likita